An tambayi Anas yaya karatun Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yake? sai ya ce: «Ya kasance yana yin madda

Daga Ƙatada ya ce: An tambayi Anas yaya karatun Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yake? sai ya ce: «Ya kasance yana yin madda», sannan ya karanta: {Bismillahir rahmanir rahim}[al-Fatiha:1] yana yin maddar Bismillah, kuma yana yin maddar Al-Rahman, kuma yana yin maddar Al-Rahim.

[Ingantacce ne] [Bukhari ne ya rawaito shi]

An tambayi Anas ibnu Malik - Allah Ya yarda da shi - yaya karatun Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - na Alƙur'ani yake? sai ya ce: Ya kasance yana jan sautinsa da karatu ja; yana jan Lami kafin Ha'i na lafazin jalalah, kuma yana jan Mim wanda ke kafin Nun daga Al-Rahman, kuma yana jan Ha'i daga Al-Rahim.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/65245